# ADDU'A

WALLAFAR
DR. ABDULMUHSIN DAN MUHAMMAD ALƘASIM
Limami kuma mai huɗuba a masallacin Annabi mai daraja

# ADDU`A

Domin sauke littafin ka bi kan wannan alamar (code)

a-alqasim.com

# ADDU`A

WALLAFAR

**DR. ABDULMUHSIN DAN MUHAMMAD ALƘASIM**

Limami kuma mai huɗuba a masallacin Annabi mai daraja

Da sunan Allah Mai rahmah Mai jinƙai

# GABATARWA

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai, kuma tsira da aminci su tabbata ga Annabinmu Muhammad da iyalansa da sahabbansa baki ɗaya.

**Bayan Haka:**

Allah Ya halicci mutane da aljanu domin bauta masa, kuma yana daga cikin falalar Allah ga halittunsa yawaita nau`oin bauta, daga cikinsu akwai abinda yake bautar zuciya ce kamar dogaro ga Allah da jin tsoron Allah, kuma daga cikinsu akwai abinda yake bauta ce ta zahiri kamar sallah da zakkah, kuma tsagwaron bauta kuma tsantsarta itace addu`a, sha`aninta a cikin addini mai girma ne, kuma nassoshi sun yawaita akan bayanin matsayinta da kwaɗaitarwa zuwa gareta da zaburarwa akanta da bayanin ladubbanta.

Kuma ita bautane wanda bayi basa wadata daga gareta komai banbancin halin da suke ciki da

matsayoyinsu, kuma duk wanda ya kasance mai tsarkake addu`arsa ga Allah, kuma mai dacewa ne da sunnar Annabinsa -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- a cikinta; to ya gabatar da bauta mai girma, kuma addu`arsa tafi kusa da a amsa masa, kuma wanda ƙafafunsa suka zamar dashi sai ya gaza acikin roƙonsa ga Allah Maɗaukaki, ko yayi ƙetare iyaka acikinta, ko zuciyarsa da ratayu da waninSa; to haƙiƙa yayi hasarar bauta mai girma, kuma bai sami abinda yake nema ba, sannan ya kai kansa zuwaga alƙawarin azabar Allah.

Kuma domin muhimmancin addu`a, da buƙatar mutane zuwa gareta; sai na rubuta acikin wannan littafin wasu darrusa da suke tattauna cewa kada a roƙa face Allah Shi kaɗai, kuma na sanya masa suna «Addu`a», asalinsa huɗuba ce dana gabatar da ita a masallacin Annabi ranar Juma`a, ashirin ga watan Safar, shekara ga dubu ɗaya da ɗari huɗu da arba`in da huɗu bayan Hijrah.

Ina roƙon Allah Ya sanya shi tsarkakakke ne domin neman yardarSa, kuma ya zama mai amfani ga bayinSa.

Kuma tsirar Allah da aminci su tabbata ga Annabinmu Muhammad da iyalansa da sahabbansa baki ɗaya.

**Dr. Abdulmuhsin Ɗan Muhammad Alƙasim**

Liman kuma mai huɗuba a masallacin Annabi.

Na kammala shi ranar ashirin ga watan Safar, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da arba`in da huɗu bayan Hijrah.

# HAƘIƘANIN ADDININ MUSULUNCI SHINE TSARKAKE AIKI GA ALLAH SHI KAƊAI

Addinin Allah wanda Ya yardar da shi ga halittunSa dukkansu, na farkonsu dana ƙarshensu shine Musulunci, annabawa sun zo dashi dukkansu, kuma manzanni dukkansu sun ɗaga tutarsa, Maɗaukakin sarki Ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلۡإِسۡلَٰمُ ﴾

{lallai addini a wurin Allah shine Musulunci} [Aali-Imraan: 19], kuma shine tsarkake aiki ga Allah Shi kaɗai, da miƙa wuya gareShi matsayin Ubangiji, Mamallaki, Mai gudanarwa, kuma Allah Abin bautawa Shi kaɗai banda waninSa, kuma shine miƙaƙƙiyar hanya addinin babanmu Ibrahim, -aminci ya tabbata a gareshi-

﴿ ثُمَّ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ أَنِ ٱتَّبِعۡ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۖ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ﴾

{sannan Muka yi wahayi a gareka cewa kabi hanyar Ibrahim miƙaƙƙiya kuma bai kasance daga cikin masu shirka ba}[An-nahl:123], kuma shi aƙida ce kuma da kuma shari`ah, kuma ilmi ne da aiki, kuma zahiri ne wanda yake gasgata ɓoye.

Kuma kalmar «babu abin bautawa da gaskiya sai Allah» itace tushensa da kuma asalinsa, da kuma farko da ƙarshensa, da sababinsa da manufarsa, da kuma ƙubbar gininsa wacce da itane cikarsa da kyawunsa,

Kuma ma`anarta daga lafazinta yana matsayin rai ne ga gangar-jiki, ba'a amfana da jiki ba tare da rai ba, kuma furtata ba tare da ƙudurce ma'anarta ba; baya amfanar da ma'abocinta da komai.

Kuma ita kalma ce wacce ta ƙunshi addini dukkansa, wanda ya faɗe ta tare da sanin ma'anarta, yana mai aiki da abinda take nunarwa, yana mai cika hakƙoƙinta; to haƙiƙa ya tattabatar da tauhidi, kuma wanda ya tabbatar tauhidi kamar yadda Allah farlanta masa zai shiga aljannah ba tare hisabi ko azaba ba.

# ADDININ MUSULUNCI YA GINU A BISA ROƘON ALLAH SHI KAƊAI

Mafi gaskiyar hujjar daga bawa gameda tauhidi, kuma mafi cikan dalili akan keɓantar Mahalicci da kaɗaici; shine roƙon Allah Shi kaɗai banda waninSa, Annabi -Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Idan zaka roƙa to ka roƙi Allah**» [Timizi ya ruwaito shi][1] .

Kuma addinin Allah baya tsayuwu sai dai abisa kaɗaita Allah da roƙo banda waninSa, kuma da wannan ne ya aiko manzanninSa, kuma ya saukar da littattafanSa, kuma shine addininSa da yake so bayinSa su bayyana shi koda cikin hakan akwai turmusa hancin masu kauda kai daga gare shi.

﴿ فَٱدۡعُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡكَٰفِرُونَ ﴾

{Sabõda haka ku kirãyi Allah, kunã mãsu tsarkake addini a gare Shi, kuma kõ dã kãfirai sun ƙi} [Gaafir: 14], kuma Allah Ya umurci AnnabinSa -

(1) lamba ta (2516), daga hadisin Ɗan Abbas Allah Ya kara masu yarda.

tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- da ya sanar da mutanensa cewa saƙonsa ya tsayu ne a bisa kaɗaita Allah cikin addu'a

﴿ قُلۡ إِنَّمَآ أَدۡعُواْ رَبِّي وَلَآ أُشۡرِكُ بِهِۦٓ أَحَدٗا ﴾

{Ka ce: "lna kiran Ubangijina ne kawai, kuma bã zan tãra kowa da Shi ba"} [Al-jinn: 20].

# UƘUBAR WANDA YAYI GIRMAN KAI GA ROƘON ALLAH SHI KAƊAI

Wanda yayi girman kai ga rokon Yayi masa alƙawarin wuta da ƙasƙanci,

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسۡتَكۡبِرُونَ عَنۡ عِبَادَتِي سَيَدۡخُلُونَ جَهَنَّمَ دَاخِرِينَ﴾

[Lallai waɗannan da ke kangara daga barin bauta Mini, za su shiga Jahannama sunã ƙasƙantattu"} [Gaafir: 60], kuma duk wanda ransa ya ƙyamaci rokon Allah Shi kaɗai kuma bai sami buɗin ƙirji ba sai acikin roƙon abin halitta, to wannan alama ce ta bata da rafkana daga lahira. Wanda tsarki ya tabbata a gare Shi Yace:

﴿وَإِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَحۡدَهُ ٱشۡمَأَزَّتۡ قُلُوبُ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ﴾

{Kuma idan aka ambaci Allah Shi kaɗai zukãtan waɗanda ba su yi ĩmãni ba da Lãhira zasu ƙyamata} [Azzumar: 45]. Wato: sai zukatansu su gudu kuma suyi girmankai, kuma suƙi yarda da kaɗaita Allah Shi kaɗai da bauta da addu`a.

# ADDU`A ITACE BAUTA

Babu wani matsayi na imani da Allah Ya wajabta shi ga zukata face addu'a yana lizimtashi, kuma ibadun bayyane dana ɓoye dukkansu addu'a ne ga tuƙewarsu da kuma ma'anarsu, duk wanda yayi sallah ko azumi ko hajji ko yayi sadaka; to yana rokon Ubangijinsa ne a aiwace, Bautarsa ga Ubangijinsa, da ƙanƙan da kansa gare Shi, da sonSa a gare Shi, Suna kiransa da cewa shi ɗin mai roƙon amsawa ne daga Ubangijinsa, mai neman kusa-kusa da kusanci zuwa gare Shi, to addua itace bauta da kuma ƙwaƙwalwarta da kuma tsagwaronta da kuma haƙiƙaninta. Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**lallai addua itace ibada sannan ya karanta**».

﴿ وَقَالَ رَبُّكُمُ ٱدۡعُونِيٓ أَسۡتَجِبۡ لَكُمۡۚ ﴾

**{"Kuma Ubangijinku ya ce: "Ku roƙe Ni in amsa muku"}** [Gaafir: 60] [ Ahmad ya ruwaito shi][1] .

(1) lamba ta (18432), daga hadisin An-nu`maan ɗan Bashir Allah Ya yarda dasu.

# MUHIMMANCIN ROƘON ALLAH SHI KAƊAI

Kuma saboda girman al`amarin addu`a da babban matsayinta; Allah Ya fara littafinSa da addu`a

﴿ٱهۡدِنَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلۡمُسۡتَقِيمَ﴾

{Ka shiryar damu hanya madaidaiciya} [Al-fatihah: 6], kuma Ya kammala shi da surori biyu na neman tsari waɗanda acikinsu akwai addu`a, kuma Allah Ya kira addu`a da sunan addini sai Ya ce:

﴿ فَٱدۡعُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ ﴾

{Sabõda haka ku kirãyi Allah, kunã mãsu tsarkake addini a gare Shi} [Gaafir: 14], kuma Ya kira ta da sunan bauta dukkanta sai Yace:

﴿ وَقَالَ رَبُّكُمُ ٱدۡعُونِيٓ أَسۡتَجِبۡ لَكُمۡۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسۡتَكۡبِرُونَ عَنۡ عِبَادَتِي سَيَدۡخُلُونَ جَهَنَّمَ دَاخِرِينَ ﴾

{"Kuma Ubangijinku ya ce: "Ku kira Ni in amsa muku. Lallai waɗannan da ke kangara daga barin bauta Mini, za su shiga Jahannama sunã ƙasƙantattu."} [Gaafir: 60].

# ROƘON ALLAH SHI KAƊAI ALAMA CE TA IMANI

Tsarkake Allah Shi kaɗai a cikin addu`a alamace ta imani, kuma dalilin yaƙini ne, kuma igiyar tsira ce, kuma hanyar cin nasara ce da tsira, kuma shine taken Annabawa da muminai, saboda haka mai addu`a wanda yake kaɗaita Ubangijinsa acikin addu`arsa shine mai bauta da gaskiya, kuma masani wanda ya dace da hanyar mafi darajar gaskiya, don haka addu`a itace rukuni mafi ƙarfi wanda musulmai suke komawa zuwa gare shi, kuma mafaka mafi aminci wacce mabuƙata suke fakewa dashi, kuma masifu da tsanance-tsanance suna sanar da bawa Ubangijinsa, kuma suna kama hannunsa zuwa ga yin ikhalasi a cikin addu`arsa,

﴿ وَإِذَا مَسَّ ٱلْإِنسَٰنَ ٱلضُّرُّ دَعَانَا لِجَنۢبِهِۦٓ أَوْ قَاعِدًا أَوْ قَآئِمًا ﴾

{Kuma idan cũta ta shãfi mutum, sai ya kirãye Mu, yanã (kwance) ga sãshensa kõ kuwa zaune, kõ kuwa a tsaye} [Yunus: 12].

# ALLAH SHI KAƊAI YAKE AMSA ADDU`OI

Ubangijinmu Tsarki ya tabbbata a gare Shi ana kiranSa Shi kaɗai acikin kowane lokaci da yanayi; kuma Shine Mahalicci wanda baya gazawa daga yin wani abu, kuma Mai iko Mai Tanƙwarawa wanda Ya ɗaukaka saman komai, arziki a hannunSa yake, kuma kyauta da hanawa daga gare shi suke kuma zuwa gare Shi, kuma siffofin cika da kyawu da girma siffofin ne na gaskiya waɗanda basa rabuwa da Shi, kuma duk wanda yayi tawassuli zuwa gare Shi da sunayenSa da siffofinSa Zai bashi abin nemansa

﴿ وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَاۖ ﴾

{kuma Allah Yana da sunaye kyawawa to ku kira Shi da su} [Al-a`raaf: 180] Ubangijinmu Shine na kusa ga masu roƙonSa da masu bautarSa, wanda ya miƙa buƙatarsa zuwa gareShi daga cikinsu zai biya masa ita, kuma wanda ya roƙeShi zai bashi, kuma wanda ya miƙa talaucinsa zuwa gareShi zai wadatar dashi

﴿وَإِذَا سَأَلَكَ عِبَادِي عَنِّي فَإِنِّي قَرِيبٌ ۖ أُجِيبُ دَعْوَةَ ٱلدَّاعِ إِذَا دَعَانِ ۖ﴾

{"kuma idan bayina suka tamabayeka gameda Ni to Ina kusa, ina amsa kiran mai kira idan ya kiraNi"} [Baƙarah: 186].

Shine Rayayye Tsayayye wanda yake riƙe da komai wanda ya kira Shi zai fuskanci Ubangiji ɗaya ne Abin nufi da buƙatu Mai iko akan yaye baƙinciki

﴿هُوَ ٱلْحَيُّ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱدْعُوهُ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ ۗ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ﴾

{Shine Rayayye babu abin bauta da gaskiya face Shi to ku kira Shi kuna masu tsarkake addini a gare Shi} [Gaafir: 65], kuma kaɗaituwarSa da cancantar addu`a banda waninSa hujja ce akan cewa Shine Gaskiya Shi kaɗai, kuma roƙon waninSa ba`a amsata, Wanda al`amarinSa ya girmama Ya ce

﴿لَهُۥ دَعْوَةُ ٱلْحَقِّ ۖ وَٱلَّذِينَ يَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَسْتَجِيبُونَ لَهُم بِشَيْءٍ﴾

{kiran gaskiya gare Shi yake kuma waɗanda suke kiran waninSa basa amsa masu da wani abu}[Ar-ra`ad: 14], kyautarSa na ba ƙwaƙwale

mamaki, kuma karamcinSa babban abin mamaki ne, Yana sakayya da alkhairai masu yawa akan ƙanƙanin aiki mai kyau, kuma duk wanda ya yabeShi kuma ya kyautata roƙonSa Zai bashi abin nema gwag-gwaɓa, kuma Yana yafe manyan zunubai ga wanda addininsa ya inganta da tauhidinsa, kuma bai haɗa Shi da wani tare daShi ba, Wanda tsarki ya tabbata a gare Shi Ya ce acikin hadisi ƙudsi: «**Duk wanda ya haɗu da Ni da cikin ƙasa na kusakurai -wato zunubbansa sun cika ƙasa ko kuma sun kusa cikinta- kuma baya haɗa Ni da wani abu Zan haɗu dashi da kwatankwacinta na gafara**» [Muslim ya ruwaito shi][1] .

(1) lamba ta (2687), daga hadisin Abu Zharr Allah Ya yarda da shi.

# ANNABAWA ALLAH SUKE ROƘO SHI KAƊAI

Mafiya soyuwar halittu a wurin Allah sune waɗanda suka fi yawan roƙo da yawan naci, kuma duk sanda imanin bawa ya ƙaru da fahimtarsa ga addininsa da ratayuwarsa ga Ubangijinsa; kwaɗayinsa ga addu`a zai ƙaru acikin duk halin da yake ciki, Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Ɗayanku ya tambayi Ubanjinsa dukkan buƙatunsa; har ya roƙi igiyar takalminsa idan ta tsinke**» maɗaurin takalminsa: shine ɗaya daga cikin igiyoyin takalminsa, [Tirmizi ya ruwaito shi][(1)] , Shehun Musulunci ya ce: «Annabawa da mabiyansu basu gushe ba suna rokon Allah maslahar addininsu da duniyarsu da lahirarsu, to wanene wanda ya wadatu daga roƙon Allah Maɗaukaki?! Kuma abinda bawa ya keɓanta dashi shine ya roƙi Ubangijinsa, kuma abinda Ubangijin ya keɓanta dashi shine Ya amsa masa, to duk wanda yayi zaton cewa zai wadata daga roƙonSa to haƙika

(1) lamba ta (8-3604), daga hadisin Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi.

ya fita daga ɗaurin bauta». Ya fita daga ɗaurin bauta: wato ya rabu da ita[1] .

Kuma annabawan Allah sha`aninsu shine yawan addu`a aduk yanda yanayi ya canza,

﴿إِنَّهُمۡ كَانُواْ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَيَدۡعُونَنَا رَغَبٗا وَرَهَبٗاۖ وَكَانُواْ لَنَا خَٰشِعِينَ﴾

{lallai su sun kasance suna rige-rige da juna cikin alkhairai kuma suna kiranMu cikin kwaɗayi da tsoro kuma sun kasance masu tsoronMu} [Al-anbiya`: 90], zuciyar Zakariyya -aminci ya tabbata a gare shi- ta kamu da son ɗa sai ya roƙi Ubangijinsa zuriya ta gari, kuma ya yabi Ubangijinsa sai yace:

﴿إِنَّكَ سَمِيعُ ٱلدُّعَآءِ﴾

{Lallai Kai Mai jin addu`a ne} [Aali-Imraan: 38], sannan ya tashi zuwa mihrabinsa sai ga mala`iku suna masa albishirin Annabi daga tsatsonsa, tare yawan shekarunsa da raunin ƙashinsa,

(1) Arraddu alash-shazili (shafi na 57).

kuma mutanen Nuhu sun fuskanci Annabinsu da saɓawa da ƙaryatawa,

﴿ فَدَعَا رَبَّهُۥٓ أَنِّي مَغۡلُوبٞ فَٱنتَصِرۡ ﴾

{sai ya kira Ubangijinsa cewa anyi rinjaye akaina to Ka taimakeni} [Al-ƙamar: 10], sai Allah Ya nutsar da waɗanda ke doronƙasa acikin Ɗufanu mai girma banda waɗanda suka bishi daga cikin muminai, kuma Allah Ya bada labarin ma`abota kogo cewa su matasa ne masu kaɗaita Allah sun san cewa roƙon Allah Shi kaɗai shine addinin da Allah baYa karɓan waninsa, sai suka tashi acikin mutanensu suka ce:

﴿ رَبُّنَا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ لَن نَّدۡعُوَاْ مِن دُونِهِۦٓ إِلَٰهٗاۖ

لَّقَدۡ قُلۡنَآ إِذٗا شَطَطًا ﴾

{Ubangijinmu shine Ubangijin sammai da ƙasa bazamu kira wani koma bayansa matsayin abin bauta ba, lallai ne don haka mun faɗi abinda ya ƙetare haddi} [Al-kahf: 14], kuma abin maimaitawar muminai cikin gyaffai na wuni da kafin alfijir,

﴿تَتَجَافَىٰ جُنُوبُهُمۡ عَنِ ٱلۡمَضَاجِعِ يَدۡعُونَ رَبَّهُمۡ خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَمِمَّا
رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ﴾

{Sãsanninsu nã nĩsanta daga wurãren kwanciya, sunã kiran Ubangijinsu bisa ga tsõro da tsammãni, kuma sunã ciryawa daga abin da Muka azurta su} [As-sajda: 16 ], kuma yawaita zama tare da wanda yake yawan rokon Ubangijinsa kuma yana mai tsarkake ayyukkansa gareShi; yana daga cikin abinda Allah Ya umurci AnnabinSa

﴿وَٱصۡبِرۡ نَفۡسَكَ مَعَ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ رَبَّهُم بِٱلۡغَدَوٰةِ وَٱلۡعَشِيِّ يُرِيدُونَ وَجۡهَهُۥ﴾

{Ka haƙurtar da ranka tãre da waɗanda ke kiran Ubangijinsu, sãfe da maraice, sunã neman yardarSa} [Al-kahf: 28].

# AMFANONIN ROƘON ALLAH SHI KAƊAI

Amfanin addu'a yana da girma, kuma alkhairinsa gamamme ne, yana amfanarda rayayyu da matattu, mai addu'a da wanda aka yi ma addu'ar suna samin albarkarsa, kuma shi sababi ne mai tasiri kamar sauran sabubba, bawa yana rokon Ubangijinsa da ƙaddarawar Allah, kuma ana karɓa masa da ganin damar Allah, Ita addu'a tana kauda bala'i idan ilmin Allah ya gabaci haka, kuma tana janyo alkhairi kuma tana tseratarwa daga halaka da izinin Allah, to duk al'amarin daga Allah yake kuma zuwa gare Shi yake, babu iko ga wani halitta zuwa gare Shi.

Kuma roƙon Allah tsantsa fitilla ce mai haskawa, baya barin kishiya ko abokin karo, ko abokin tarayya ko mataimaki, ko wani abin bauta ko wani Ubangiji face Allah Shi kaɗai, kuma dashine mai addu`a yake zama bawa ga Ubangijinsa, sai ya kadaitaShi da nufata da girmamawa da so, da tsoro da fata, sai zuciya ta rataya da Shi a yanayin farin ciki da damuwa, kuma harshe ya riƙa ambatonSa da addu'a cikin kwanciyar hankali da baƙin ciki.

# DAGA CIKIN ALAMOMIN MAI KAƊAITA UBANGIJINSA

Wanda yaso sanin haƙiƙanin tauhidinSa to ya dubi cewa wanene yake roƙo? Duk wanda ya tsarkake addu'arsa ga Allah to ya dace da tauhidi, kuma duk wanda ya kira wanin Allah ya awka cikin shirka, Wanda tsarki ya tabbata a gare Shi Ya ce:

﴿وَمَن يَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ لَا بُرۡهَٰنَ لَهُۥ بِهِۦ فَإِنَّمَا حِسَابُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦٓۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلۡكَٰفِرُونَ﴾

{Kuma wanda ya kira, tãre da Allah, wani abũn bautãwa na dabam, bã yanã da wani dalĩli game da shĩ (kiran) ba, to hisãbinsa yanã wurin Ubangijinsa kawai. Lallai ne, kãfirai bã su cin nasara} [Al-mu'minuun: 117].

# MANZANNI BASU UMURCI WANI CEWA YA ROƘE SU BA

Cika da girma ga Allah suke Shi kadai, kuma bauta bata dacewa sai dai ga Allah, Kuma Allantaka bata dace ba sai ga girmanSa, kuma babu cikin mutane duk yanda matsayinsu ya kai wanda ya cancanci a roƙeshi komabayan Allah domin abu mai yawa ko dan kaɗan, to wanda ya gaza halittar ɗan ƙanƙanin halitta a wannan duniyar; to bashi da rabo acikin bauta da addu'a

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَن يَخۡلُقُواْ ذُبَابٗا وَلَوِ ٱجۡتَمَعُواْ لَهُۥۖ﴾

{Lallai ne waɗanda kuke kira baicin Allah, bã zã su halitta ƙudã ba, kõ da sun tãru gare shi} [Al-hajj: 73], kuma Allah Ya zabi Manzanni da cikin halittunSa kuma Ya fifitasu akan wasunsu kuma babu wani cikinsu da yayi jayayya da Allah cikin UbangijintakarSa, ko ya umurci mutane su roƙeshi ko ya yarda da hakan

﴿وَإِذْ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ءَأَنتَ قُلْتَ لِلنَّاسِ ٱتَّخِذُونِى وَأُمِّىَ إِلَٰهَيْنِ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۖ قَالَ سُبْحَٰنَكَ مَا يَكُونُ لِىٓ أَنْ أَقُولَ مَا لَيْسَ لِى بِحَقٍّ﴾

{Kuma a lõkacin da Allah Ya ce: "Yã Ĩsã ɗan Maryama! Shin, kai ne ka ce wa mutãne, 'Ku riƙe ni, ni da uwata, abubuwan bautãwa biyu, baicin Allah?" (Ĩsã) Ya ce: "Tsarkinka yã tabbata! Bã ya kasancewa a gare ni, in faɗi abin da bãbu wani hakki a gare ni} [Al-ma'idah: 116], kumA sun kasance rashin lafiya na samunsu, da rauni; cikinsu akwai wanda aka kasha shi, da wanda yayi rashin lafiya da wanda aka yiwa sihiri, kuma su mutane ne suna ci kuma suna sha, to ta yaya wanda baya rayuwa sai da cin abinci zai kasance Allah abin bauta?!

Banda haka ma fiyayyen halitta Annabinmu Muhammad -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- an karya hakoransa na gaba kuma aka masa rotse a kai(1) , kuma ya fado daga kan doki, kuma ya

(1) Bukhari lamba ta (2911), Muslim lamba ta (1790), daga hadisin Sahl ɗan Sa`ad Allah Ya yarda dashi.

kukkuje gefensa, -wato fatarsa ta tsats-tsage- kuma yayi sallah a zaune saboda faɗowar da yayi[1] .

(1) Bukhar lamba ta (689), Muslim lamba ta (411), daga hadisin Anas ɗan Malik Allah Ya yarda dashi.

# ROƘON WANIN ALLAH SHINE ZUNUBI MAFI GIRMA A BAYAN ƘASA

Roƙon wanin Allah laifi ne mai girma, Allah Maɗaukaki Ya cewa AnnabinSa -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-

﴿وَلَا تَدۡعُ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكَ وَلَا يَضُرُّكَ فَإِن فَعَلۡتَ فَإِنَّكَ إِذٗا مِّنَ ٱلظَّٰلِمِينَ﴾

{ "Kuma kada ka kirãyi, baicin Allah, abin da bã ya amfãnin ka kuma bã ya cũtar ka. To, idan ka aikata haka, to lallai kai, a lõkacin, kanã daga mãsu zãlunci."}[Yunus:106], kuma daga cikin mafiya girman nau'ikansa; sanya wasu tsakanin Allah da bayinSa, Shehun Musulunci -Allah ya jiƙansa- ya ce: «Ba wani daga cikin Annabawa da ya sunnatawa halittu cewa su nemi addu'a ko ceto daga wurin bayin Allah na gari matattu ko wanda bashi nan ko mala'iku, bal ma wannan shine asalin shirka, domin

mushrikai kaɗai sun rike sune a matsayi masu ceto, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَيَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَضُرُّهُمۡ وَلَا يَنفَعُهُمۡ وَيَقُولُونَ هَٰٓؤُلَآءِ شُفَعَٰٓؤُنَا عِندَ ٱللَّهِۚ﴾[1]

{Kuma sunã bautã wa, baicin Allah, abin da bã ya cũtar dasu kuma bã ya amfãninsu, kuma sunã cẽwa: "Waɗannan ne macẽtanmu a wurin Allah} [Yunus: 18 ], kuma mafi girman zunubi a doron kasa shine kiran wanin Allah tare daShi, Ibn Mas'uud Allah Ya yarda dashi ya ce: «Nace ya Manzon Allah wane zunubi ne mafi girma? Yace: **Ka sanya ma Allah kishiya alhali Shi Ya halicceka**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi][2] , kuma Allah Yayi alƙawarin azaba ga wanda ya kira waninSa tare da Shi. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿فَلَا تَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُعَذَّبِينَ﴾

{Sabõda haka, kada ka kira wani abin bautãwa na dabam tãre da Allah, sai ka kasance daga

(1) Ƙaida Adheemah (1/121).
(2) Bukhar lamba ta (4477), Muslim lamba ta (86).

waɗanda ake yi wa azãba.} [Ash-shua'ra: 213], Ibn Abbas -Allah Ya yarda dashi- ya ce: yana yima waninsa gargadi ne yana cewa: «Kaine mafi karamcin halittu a wuri na da zaka riki wani abin bauta koma bayana da na azabtar da kai»(1) .

Kuma ba'a shar'anta sallah da ruku'i da sujjada ba kuma ba'a gina masallatai a ƙasar Allah ba face domin a kira Allah acikinsu Shi kadai kuma ba za'a kira waninSa ba har abada, Allah Mai buwaya da daukaka Ya ce:

﴿ وَأَنَّ ٱلۡمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدۡعُواْ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدٗا ﴾

{"Kuma lallai ne wurãren sujada na Allah ne, saboda haka kada ku kira kõwa tãre da Allah (da su, a cikinsu)." } [ Al-jinn: 18].

(1) Tafsirul Bagawi (3/480).

# MATACCE BAYA JIN MAI ROƘONSA

Mai addu'a yana rokon Mahaliccine amma kada ya roki abin halitta irinsa ba, kuma ba zai nemi ɗaukin wanda yake tarayya dashi wajen bautaba, Allah Mai buwaya da ɗaukaka Ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ عِبَادٌ أَمۡثَالُكُمۡۖ فَٱدۡعُوهُمۡ فَلۡيَسۡتَجِيبُواْ لَكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ﴾

{Lallai ne waɗannan da kuke kira, baicin Allah, bãyĩ ne misãlanku: to, ku kirãye su, sa'an nan su amsa muku, idan kun kasance mãsu gaskiya ne!} [Al-a'raaf: 194], kuma wanda yake cikin ƙabari baya jin mai kiransa koda ya kai shi matsayin Ubangijintaka, kuma baya mallakar komai ga mai neman ɗaukinsa koda ya jingina masa keɓantattu siffofin Allantaka

﴿ وَٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمۡلِكُونَ مِن قِطۡمِيرٍ ❋
إِن تَدۡعُوهُمۡ لَا يَسۡمَعُواْ دُعَآءَكُمۡ وَلَوۡ سَمِعُواْ مَا ٱسۡتَجَابُواْ لَكُمۡۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ
يَكۡفُرُونَ بِشِرۡكِكُمۡۚ وَلَا يُنَبِّئُكَ مِثۡلُ خَبِيرٖ ﴾

{kuma waɗanda kuke kira waninSa bã su mallakar kõ fãtar gurtsun dabĩno. Idan kun kira su, bã zã su ji kiranku ba, kuma kõ sun jiya, bã zã su amsa muku ba} [ Faaɗir: 13-14], Al-ƙiɗmir: Shine ɓawon dake tsakanin ƙwallo da tsokar dabino.

Kuma matatttu masu gazawane daga agazawa kansu, to ba zai yiwu su agazama waninsuba, Wanda tsarki ya tabbata a gare Shi Ya ce:

﴿وَٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَسۡتَطِيعُونَ نَصۡرَكُمۡ وَلَآ أَنفُسَهُمۡ يَنصُرُونَ﴾

{"Kuma waɗanda kuke kira, baicinSa, bã su iya taimakõn ku, kuma kansu ma, bã su iya taimaka."} [Al-a'raaf: 197].

# MAI ROƘON WANIN ALLAH YANA DA YAƘININ CEWA SHI BAYA JI BAYA AMFANARWA

Mai kiran wanin Allah yanada yaƙinin cewa wanda ya kirashi baya jin kiransa kuma ba zai amfaneshi ba, Allah Maɗaukaki Ya ce: Ibrahim ya cema mutanensa gameda gumakansu

﴿ هَلۡ يَسۡمَعُونَكُمۡ إِذۡ تَدۡعُونَ ۞ أَوۡ يَنفَعُونَكُمۡ أَوۡ يَضُرُّونَ ۞

قَالُواْ بَلۡ وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا كَذَٰلِكَ يَفۡعَلُونَ﴾

{.... Ya ce: "Shin, sunã jin ku, a lõkacin da kuke kira?" "Kõ kuwa sunã amfãnin ku, kõ sunã cũtar ku?" Suka ce: "Ã'a mun sãmĩ ubanninmu, kamar haka ne suke aikatãwa"} [ Ash-shua'ra: 72-74].

Ibn Katheer Allah Ya jiƙansa ya ce: «yana nufin: cewa sun yi iƙirarin cewa gumakansu basu yin wani abu daga cikin waɗannan, kaɗai sunga iyayensu haka suke aikatawa ne»[1] .

(1) tafseer Ibn Katheer (6/146).

# ROƘON WANIN ALLAH BA KOMAI CIKINSA SAI WAHALA DA LALATA ADDINI

Wanda ya kira matacce yana fatan samun amfani daga wurinsa ko kauda cuta; to ba abinda zai samu tare da lalacewar addini face gajiya, Wanda sha'aninsa ya girmama Ya ce:

﴿يَدۡعُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَضُرُّهُۥ وَمَا لَا يَنفَعُهُۥۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلضَّلَٰلُ ٱلۡبَعِيدُ ۝ يَدۡعُواْ لَمَن ضَرُّهُۥٓ أَقۡرَبُ مِن نَّفۡعِهِۦۚ لَبِئۡسَ ٱلۡمَوۡلَىٰ وَلَبِئۡسَ ٱلۡعَشِيرُ﴾

{Yanã kiran baicin Allah, abin da bã ya cũtarsa da abin da bã ya amfãninsa! waccan ita ce ɓata mai nĩsa. Yanã kiran wanda yake lallai cũtarwarsa ce mafi kusa daga amfãninsa! Lallai ne, tir da shi ya zama majiɓinci, kuma tir da ya zama abõkin zama!} [ Al-hajj: 12-13], kuma waiwayawar mai addu`a zuwa ga halittu, da neman ɗauki wajen rayayyu da matattu, wulaƙanta raine da ƙasƙantar da ita, Imam Ahmad -Allah Ya jiƙansa ya ce: «Ya Allah kamar yadda Ka tsare fuskata daga yin sujjada ga waninKa;

to ka tsare ta daga roƙon waninKa, kuma ba wanda zai iya yaye cuta da jawo amfani koma bayanKa»[1] .

(1) Jaami`ul uluumi wal hikam (1/481).

# DUK WANDA YA ROƘI WANIN ALLAH DON YAYE BAƘINCIKI ALLAH ZAI MASA UƘUBA DA BAƘINCIKI MAFI TSANANI

Babu wani bawa da zai kira wanin Allah ko kuma zuciyarsa ta waiwaya zuwa ga waninSa, ko kuma shaiɗan yayi masa waswasin rataya da wanin Ubangijinsa; face abinda zai same shi na tsanani da baƙinciki zai nuna masa gazawar wanda ya kira kuma zai bayyana masa rauninsa da rashin karfinsa, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ قُلۡ أَرَءَيۡتَكُمۡ إِنۡ أَتَىٰكُمۡ عَذَابُ ٱللَّهِ أَوۡ أَتَتۡكُمُ ٱلسَّاعَةُ أَغَيۡرَ ٱللَّهِ تَدۡعُونَ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ۞ بَلۡ إِيَّاهُ تَدۡعُونَ فَيَكۡشِفُ مَا تَدۡعُونَ إِلَيۡهِ إِن شَآءَ وَتَنسَوۡنَ مَا تُشۡرِكُونَ ﴾

{Ka ce: "Shĩn, kun gan ku, idan azãbar Allah ta zo muku, kõ Sã'ar Tashin Kiyãma ta zo muku, shin wanin Allah kuke kira, idan dai kun kasance mãsu gaskiya?" "Ã'a, Shĩ dai kuke kira sai Ya kuranye

abin da kuke kira zuwa gare Shi, idan Ya so, kuma kunã mantãwar abin da kuke yin shirkin tãre da shi"} [ Al-an'aam: 40-41].

Kuma duk wanda ya san kaɗaituwar Allah da mulki da wadatuwarSa daga halittu; zai yanke ƙauna daga samun amfani sai dai daga wurinSa, kuma fatansa zai yanke face awurinSa

﴿قُلِ ٱدۡعُواْ ٱلَّذِينَ زَعَمۡتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ لَا يَمۡلِكُونَ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا لَهُمۡ فِيهِمَا مِن شِرۡكٖ وَمَا لَهُۥ مِنۡهُم مِّن ظَهِيرٖ﴾

{Ka ce: "Ku kirãyi waɗanda kuka riya (cẽwa abũbuwan bautãwa ne) baicin Allah, bã su mallakar ma'aunin zarra a cikin sammai, kuma bã su mallakarsa a cikin ƙasa kuma bã su da wani rabon tãrayya a cikinsu (sammai da ƙasa), kuma bã Shi da wani mataimaki daga gare su} [ Saba': 22 ].

# YANAYIN WANDA YA ROƘI WANIN ALLAH LOKACIN MUTUWA

Idan mutuwa ta zoma wanda ya bautawa wanin Allah tare da Shi zai barranta daga abinda ya aikata:

﴿ ٱلَّذِينَ تَتَوَفَّىٰهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ ظَالِمِيٓ أَنفُسِهِمۡۖ فَأَلۡقَوُاْ ٱلسَّلَمَ ﴾

{Waɗanda malãiku suke karɓar rãyukansu sunã mãsu zãluntar kansu. Sai suka jẽfa nẽman sulhu} [An-nahli: 28] wato: sun bayyana ji da biyayya da mika wuya suna cewa:

﴿مَا كُنَّا نَعۡمَلُ مِن سُوٓءِۭ﴾

{Ba mu kasance muna aikata wani mummũnan aiki ba}, An-nahli: 28], kuma marufin ido zai yaye daga idon dukkan mutane ranar Alƙiyama sai yaga gazawar halittu haƙiƙanin yaƙini; sannan zai ga barrantar waɗanda aka riƙa roƙa, Wanda tsarki ya tabbata a gare Shi Ya ce:

﴿حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَتۡهُمۡ رُسُلُنَا يَتَوَفَّوۡنَهُمۡ قَالُوٓاْ أَيۡنَ مَا كُنتُمۡ تَدۡعُونَ

مِن دُونِ ٱللَّهِۖ قَالُواْ ضَلُّواْ عَنَّا﴾

{har a lõkacin da ManzanninMu suka je musu, sunã karɓar rãyukansu, su ce: "Ĩnã abin da kuka kasance kunã kira, baicin Allah?" Su ce: "Sun ɓace daga gare mu} [ Al-a'raaf: 37] wato: sun tafi sun barmu saboda haka bama fatan amfaninsu, ko alkhairinsu, kuma wanda ya roƙi wanin Allah to Allah Zai yi fushi dashi kuma zai dawwamar dashi a cikin wuta, Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**duk wanda ya mutu yana kiran wani kishiya komabayan Allah zai shiga wuta**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito Shi][1] .

(1) Bukhari lamba ta (4497), Muslim lamba ta (92), daga hadisin Abdullahi ɗan Mas`ud Allah Ya yarda dashi.

# YADDA SHAIƊAN YAKE SO A ROƘI WANIN ALLAH

Addu'a bauta ce mai girma da itace mai kaɗaita Allah yake banbanta daga waninsa, kuma yana daga cikin hanyar shaiɗan mafi sauƙi wajen ɓata addinin bayi, Ibnul-ƙayyim Allah Ya jiƙansa ya ce: «Neman biyan buƙata a wurin matattu, da neman ɗauki dasu, da fuskantuwa zuwa garesu, sune asalin shirka a wannan duniyar»(1) , amma shi kuwa musulmi ya tattara zuciyarsa da bautarsa da mu'amalarsa ga Ubangijinsa Shi kaɗai, kuma yana banbancewa cikin aikinsa da nufinsa da niyyarsa da sonsa tsakanin Mai halitta da abin halitta, sai ya kiyayewa kowa haƙƙinsa da matsayinsa, bazai ba ɗayansu haƙƙin ɗayaba, Shi Ubangiji Shi ne yake da bauta, kuma shi ake roƙo, tsoro da fata gare Shi suke, su kuma halittu na kwarai ana sonsu kuma ana koyi dasu, da kiyaye mutucinsu da kuma yabo mai kyau. Allah Mai tsarki Ya ce:

(1) Madarijus salikeen (1/353).

﴿ فَأَقِمۡ وَجۡهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفٗاۚ فِطۡرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيۡهَاۚ لَا تَبۡدِيلَ لِخَلۡقِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ﴾

{Sabõda haka, ka tsayar da fuskarka ga addini, kanã mai karkata zuwa ga gaskiya, halittar Allah da Ya halitta mutãne a kanta. Bãbu musanyãwa ga halittar Allah, wannan shĩ ne addini madaidaici kuma amma mafi yawan mutãne ba su sani ba.} [Ar-ruum: 30].

# TAUHIDI SHINE MAFI DARAJAR ABINDA MUTUM YA MALLAKA

Mafi tsadar abinda aka ba bawa shine kaɗaitawarsa ga Ubangijinsa, kuma mafi girman ni'ima itace tabbatarsa akansa har ya haɗu dashi, ɗan kaɗan daga cikinsa idan ya inganta zai tseratar daga dawwama a wuta, kuma cikarsa yana hana shigarta, kuma shaiɗan yanada dabarun yaudara da shubuhohi waɗanda yake ɓatar da bayi dasu daga addininsu, kuma babu wata shubuha da take gittoma bawa face acikinta akwai abinda zai ruɗeshi ya bita, kuma ya jawoshi zuwaga gasgatata, to duk wanda yake neman tsira to ya riƙa muraji'ar tauhidinsa da imaninsa, ta hanyar karanta Alƙur'ani da nazarin ma'anoninsa da neman ƙarin ilmi, kuma ya nesanta kansa daga wuraren shubuha.

Muna Roƙon Allah ilmi mai amfani da aiki na ƙwarai da addu`a tsarkakakkiya ga Allah, kuma tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabinmu Muhammad da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

# Abubuwan da yake ciki

GABATARWA.................................................... 5
HAKIKANIN ADDININ MUSULUNCI SHINE TSARKAKE AIKI GA ALLAH SHI KAƊAI ................................... 8
ADDININ MUSULUNCI YA GINU A BISA ROKON ALLAH SHI KAƊAI.............................................10
UKUBAR WANDA YAYI GIRMAN KAI GA ROKON ALLAH SHI KAƊAI.............................................12
ADDU`A ITACE BAUTA.......................................13
MUHIMMANCIN ROKON ALLAH SHI KAƊAI ..........15
ROKON ALLAH SHI KAƊAI ALAMA CE TA IMANI ....17
ALLAH SHI KAƊAI YAKE AMSA ADDU`OI ...............18
ANNABAWA ALLAH SUKE ROKO SHI KAƊAI ..........21
AMFANONIN ROKON ALLAH SHI KAƊAI ...............25
DAGA CIKIN ALAMOMIN MAI KAƊAITA UBANGIJINSA..................................................26
MANZANNI BASU UMURCI WANI CEWA YA ROKE SU BA........................................................................27
ROKON WANIN ALLAH SHINE ZUNUBI MAFI GIRMA A BAYAN KASA ...............................................30
MATACCE BAYA JIN MAI ROKONSA .....................33

MAI ROKON WANIN ALLAH YANA DA YAKININ CEWA SHI BAYA JI BAYA AMFANARWA ................35

ROKON WANIN ALLAH BA KOMAI CIKINSA SAI WAHALA DA LALATA ADDINI................................36

DUK WANDA YA ROKI WANIN ALLAH DON YAYE BAKINCIKI ALLAH ZAI MASA UKUBA DA BAKINCIKI MAFI TSANANI ..................................................38

YANAYIN WANDA YA ROKI WANIN ALLAH LOKACIN MUTUWA .........................................................40

YADDA SHAIƊAN YAKE SO A ROKI WANIN ALLAH..42

TAUHIDI SHINE MAFI DARAJAR ABINDA MUTUM YA MALLAKA...........................................................44

Mu'assasar ɗalibul ilmi domin yaɗawa da kuma rabawa.

00966506090448




## KA KARANTA CIKIN WANNAN LITTAFIN:

- Addu'a bautace mai girma matuƙa, mai muhimmanci ce ga kowane musulmi,- kuma yin iklasi cikinta yana bayyana gwargwadon tauhidin bawa,
- Allah madaukaki yanaso daga bayinSa su roƙeShi a cikin kowane lokaci, Kuma Yana ƙin wanda yake roƙon waninSa,
- Roƙon Allah shi kaɗai na daga tafarkin Manzanni, da Kuma hanyar waliyyan Allah nagari.
- Roƙon wanin Allah daga cikin rayayyu da kuma matattu shirka ce ga Allah, kuma mai roƙo bazai amfana da ita ba.
- Mafi girman zunubi a ban ƙasa shine roƙon wanin Allah tare dashi-
- Tauhidin Allah shine mafi darajar abinda bawa ya mallaka, kuma wanda yayi shirka cikin roƙo to haƙiƙa yayi asarar tauhidi.

مترجم إلى لغة الهوسا

ردمك:

مؤسسة طالب العلم للنشر والتوزيع: ٠٥٠٦٠٩٠٤٤٨